TASIRIN MUSULUNCIA WAKOKIN BAKA NA HAUSA

Daga
Muhammad Rabi'u TAHIR
Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka
Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria.

1.0 Gabatarwa

Maƙasudin wannan takarda shi ne gabatar da bayani dangane da gudunmawar da waƙoƙin baka na Hausa suke badawa ta ɓangaren kyawawan ɗabi'un Hausawa waɗanda suka dace da Musulunci.

Waƙar baka wani katafaren tsauni ne, daga cikin tsaunukan adabi da yake ɗauke da hanyoyin ci gaban al'umma, ta fuskar al'adu da siyasa da addini da zumunci da karamci ko wani canji da ke iya samun wannan al'umma a yau. Har ila yau wannan fage na waƙar baka fage ne da ke tafiya da kusan kowane irin abu da ake nema dangane da al'ummar Hausawa.

Kusan waƙar baka abu ce wadda ke tafiya kafaɗa-da-kafaɗa da zamani ta kowace irin fuska, musamman idan an dubi yadda mawaƙan baka ke iya sarrafa basirarsu dangane da kowane irin juyin zamani kamar waƙar 'A janye akwati' da sauransu. Sannan kuma waƙoƙin ba su bar kowa da komai ba a cikin tsari da ma'ana nasu. Ganin haka ya ba wannan maƙala dama da ta yi wani tsokaci kaɗan dangane da abin da ake iya samu na tasirin Musulunci a cikin waƙoƙin baka na Hausa.

2.0 Wakar Baka

Wakar baka ta Hausa, ana fatan ta sanar da wasu ko wata al'umma abin da ba ta sani ba, musamman al'ummar Hausawa ko waninta, ko ta shiryar da mutum zuwa ga wani abin alhairi da bai san da shi ba musamman kamar wanke hannu kafin cin abinci, wanda abu ne da kusan yawan mutane sun yi watsi da haka, sakamakon amfani da cokali yau da gobe, duk da cewa abu ne mai kyau a Musulunce da al'adance. Har wa yau, wannan makala na kallon wakar baka ta Hausa a matsayin wani ginshiki na gina al'umma ta fuskar al'ada da addini. Matsayin wakar baka ta Hausa a yau ya shafi rayuwar al'umma kacokan, domin ta taɓo kusan ko'ina na rayuwar al'umma, sai dai kawai wanda ya yi wa wakar baka sanin Damisan Bunu.

Wakar baka ta Hausa tsangaya ce da ke ɗauke da ɗimbin ilmi a ɓangaren koyar da al'umma darussa mabanbanta. Haka wakar baka ta Hausa ta zama fitila mai jagorancin ci gaban al'umma da taskace adabinta da addini ta kowace fuska. Domin ana hasashe ga wakar baka ta Hausa a matsayin wani gamji wanda kowa ke shan inuwarsa. Haka mai sauraro ana hasashen ya kasance yana sauraron wakar baka ta Hausa da tunani managarci ba gurɓatacce ba, kuma ya zama mai neman sani daga cikin abin da wakar take koya masa, domin ya samu ingantacciyar rayuwa wajen iya zama da iyali ko iyaye ko shuwagabanni. Ko ba komai ana nazarin wakar ko dai domin nishaɗi ko kuma domin ilmantarwa.

Wakar baka wani katafaren fage ne da ke ƙunshe da kyawawan abubuwa na rayuwa waɗanda suke tafiya sahu-bayan-sahu da al'adun Hausawa. Irin waɗannan kyawawan sinadarai na rayuwa suna danƙare cikin wakokin baka na Hausa, waɗanda suka haɗa da kyauta da

girmama bako da aure da cimaka da sutura da sauransu. Misali, ɗauki wakar Dan Maraya Jos ka ga abin da yake cewa:

Jagora : Sai dai in wanke goma,
: In sa biyar su a ƙwaraya,
: In ɗebi duniyar al'ada,
: Shi ne abin da ni nai gado.

A wannan ɗan waka, mawakin yana magana ne, a kan abubuwa guda uku, na farko yana magana ne kan tsaftar wanke hannu a lokacin da za a ci abinci. Na biyu kuma yana magana ne a kan yin amfani da hannun dama a lokacin cin abinci. Na uku kuma shi ne yin riko da al'adu. Idan muka yi tunani tsaf za mu taras, duk waɗannan abubuwa da wannan waka take magana a kai, abubuwa ne da suke da gurbi a Musulunci. Musulunci ya kawo tsafta ce hannu kafin a yi amfani da shi a lokacin cin abinci. Sannan kuma Musulunci ne ya yi umurni da a ci abinci da hannun dama.

Ke nan wakar baka, ta shiga sahun bayyana wasu al'adun Hausawa waɗanda suka dace da addinin Musulunci ga ta dai waka ce wadda ake ganin ai ƙirarra ce, sai ga shi kuma ta tattara wasu ɗabi'u na Musulunci waɗanda suke ɗamfare da harkokin Hausawa na yau da kullum.

3.0 Nason Tubalan Musulunci a Wakokin Baka

Idan muka tsaya tsaf muka dubi wakokin baka da idon basira, za mu fahimci, suna magana ne a kan wasu tubalai da addinin Musulunci yake kira a kansu.

Alalmisali, Musulunci ya yi umurni da idan mutum ya yi bako, ya yi masa goma ta arziki wajen ba shi abinci da masauki da sauransu musamman idan zai kwana. Idan ba a manta ba, an samu hadisai daga Manzon Allah, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, kan girmama bako aiki ne na masu imani da Allah da Manzo, ka ga ke nan yi ma bako hidima, aiki ne wanda Allah yake umurni da a aikata shi, sai ga shi cikin al'adun Hausawa kamar yadda wannan waka da take tafe take cewa:

Jagora : Da munka je gidan Sardauna,
'Y/ Amshi : Kaduna mun ji dadi,
: Wurin kwana mai kyawo
: Ga gadaje na karfe,
: Katifai da matasai,
: Kujerun kwarai da fanka,
: Ga madubi mu duba,
: Wurin wanka mai kyau,
: Muna ta shagali ga fitila,
: Kana babu yunwa ba kisa,
: Goro an ka kaimun da yawa,
: Kamar huhu dai an ka aje.
(Musa Dankwairo: Wakar Sardauna)

Haka kuma a wakokin baka na Hausa za a iya kwankwance wasu dabi'u da suka dace da Musulunci, musamman a wakar Mamman Shata inda yake cewa:

Jagora : Don Salla da Salatil fati,
: Don Allah mata ku yi Aure,
'Y/ Amshi : Don Salla da Salatil fati,
: Don Allah mata ku yi Aure.

A wannan waƙa za a iya nazartar abubuwa kusan guda uku da farko akwai salla da salati ga kuma zancen aure. Idan aka ɗauki abu na ƙarshe watau batun aure wanda tun kafin Hausawa su yi cuɗanya da wasu al'ummomi suna aure a al'adance, daga bisani kuma Musulunci ya tabbatar da haka sannan kuma ga waƙar baka ta ƙara tabbatar da haka. Ke nan, an samu tarayya a kan maganar aure, yin aure Musulunci ne, sannan al'ada ce ta Hausawa a duk inda suke kuwa. Saboda haka wannan waƙar tana ɗauke da ambaton Musulunci musamman ta fuskar ƙirar waƙar, domin kuwa, ba a roƙon kowa a Musulunci sai Allah shi kaɗai. Ta fuskar ma'ana kuwa za a iya cewa, Musulmin adabi ne, domin kuwa tana nufin, mata su riƙe aure yadda ya kamata saboda Allah.

Barmani Coge, shahararriya ce kuma fitacciyar mawaƙiya ce a ƙasar Hausa, ta yi waƙoƙi da dama, waɗanda suke magana a kan ɓangarori na rayuwa daban-daban. Daga ciki akwai waƙar da ta yi a kan sana'a, kamar yadda ta ce:

Jagora : Ku kama sana'a mata,
: Macen da ba ta sana'a aura ce.

Za a iya fahimtar irin muhimmancin sana'a, ba ma kawai ga maza ba, a'a har da matan aure a gidajen mazansu. Bahaushe bai yar da da zaman banza ba, sai kuma ga shi da Musulunci ya zo sai ya ƙara tabbatar da hakan, sannan kuma ga waƙar baka ita ma ta samar da haka, duk da cewa Musulunci bai aminta da zaman kawai ba, haka wannan waƙa ta fuskar ma'ana za a iya gwamutsa ta cikin jerin waƙar baka da ta kawo abin Musulunci ya hana.

Wakar baka ta Hausa, rumbu ce wanda ke kunshe da duk wani nau'i na rayuwar bahaushe, daga ciki akwai tattali, wato tsimi da tanadi. Kamar yadda Dr. Alhaji Mamman Shata Katsina, ya ce:

Jagora : Kudi a kashe shi ta hanya mai kyau,
'Y/ Amshi : Kudi a kashe shi ta hanya mai kyau.

Daga cikin wannan waka za a iya fahimtar irin yadda tattali ke da amfani ga rayuwar Bahaushe, Musulunci kuma ya kara tabbatar da hakan. Ku san a iya cewa tsimi ko tsururi da tattali, dabi'a ce ta Hausawa wajen ganin an kiyaye hakkokin iyali da makwabta da kuma mabarata, wanda hakan Musulunci ne, da haka a iya bugun-gaba da cewa har ma akwai in da Allah ya yi magana kan yin tattali da kuma hani da almubazzaranci, ka ga ke nan yin tattali kamar yadda waccen waka ta nuna Musulunci ne.

Kar fa a manta wakar baka ke baje-kolin kabakin da take dauke da shi, yana da kyau a nazarci adabi ta fuskoki guda biyu , musamman wakar baka ta Hausa ta fuskar nishadi da kuma ilmi, wanda hakan zai haifar da amfani mai gwabi ta fuskokin rayuwar al'umma, a yanzu idan aka dubi wakar baka ta fuskar ilimi, Garba Maitandu Shinkafi cewa ya yi:

Jagora : Duk wanda yaz zam ba shi da ilimi,
'Y/ Amshi : Ba mu dai ga cin riba tai ba,
: Da shi da Jaki, mi zai raba su,
: In ba zancen rashin bindin nan ba.
(Wakar Jaki : Garba Maitandu Shinkafi)

Ta yin la'akari da wannan wakar, an fahinci, muhimmancin ilmi na da yawa daga cikinma'anonin wakar, baya ga haka idan aka

dubi bayanin ta fuskar addini wanda Musulunci yana magana kan neman ilimi tun daga haihuwa har zuwa mutuwa. Sai ga bayani ya koro ta kirar wakar baka, ta girmama ilmi da mai shi, sannan duk wanda ba shi da ilimi an kwatanta shi da jaki, wanda bai san ciwon kansa ba. Wannan ya nuna cewa adabin Hausawa ya ba ilmi wani babban gurbi wanda hakan ya dace da abin da Musulunci yake fadakarwa da a nema, tun daga farkon rayuwa har zuwa komawa ramin gaskiya.

Alhaji Shehu Ajilo Danguzuri, ya nuna martaba da mahimmanci rike aure ga al'ummar Hausawa, a cikin wannan wakar in da ya ce:

Jagora : Wanda ba ya noma, nan duniya,
: Ko da rikon aure zai mai wuya.
(Shehu Ajilo: Wakar Noma)

A cikin wannan wakar akwai maganar noma, wanda ita ce hanyar samar da abinci ga iyali a gida. Musulunci ya tabbtar da cewa, hakkin maigida ne ya ciyar da iyalansa, kuma ga shi noma babbar hanya ce ta samar da abinci ga bahaushe, tun kafin zuwan Musulunci. Da Musulunci ya zo kasar Hausa, sai ya tabbatar da haka, bugu da kari kuma sai wakar baka ta dada fito da bayani fili yadda zai taimaka wa al'umma su fahimci ciyar da iyali abu ne muhimmi, duk da cewa sun san hakan, amma ai sabunta karatu ba zai za ma laifi ba. Alhaji Sani Sabulu Kanoma yana cewa:

Jagora : Mai dadiro ɓatacce ga Allah,
: Mai dadiro rashi yai mai oba,
: Mai dadiro maƙocin kura ne,
: Girma yake yana kwana daji,
: Ba duniya, ko a kiyama,
: Wurin zamanka na nan yai muni.
(Waƙar Maidadiro: Sani Sabulu Kanoma)

Za a iya fahimtar abubuwa da yawa a cikin wannan waƙar, tun farko an nuna mummunan hali da yanayi na mai yin dadiro kusan a iya cewa wannan kalma ba da daiyar kalma ba ce, dadiro ba ɗabi'a ce ta Hausawa tun asali ba, waƙar ta yi nuni da cewa ya ɓace daga tafarkin gaskiya, kuma Allah ba ya tare da shi. Bahaushe bai yarda da lalacewa ba, musamman irin ta dadiro ko akasin haka. Sai kuma ga shi Musulunci ya hana gaba ɗaya. Abu na biyu shi ne, rashi irin na talauci, domin kuwa duk mai fasiƙanci to, ba zai zauna da arziki ba, kamar yadda Musulunci ya nuna cewa, yana sa talauci, dama kuma can Bahaushe yana tabbacin cewa, yana sa talauci da kuma kyamatar wannan ɗabi'a. Kusan da ɗabi'ar Musulunci da ta Hausawa duk sun ƙyamaci wannan nau'in hali.

Har ila yau, idan aka dubi waƙar Muhammadu Gambu, nan za a iya samun misali daga cikin waƙarsa in da yake cewa:

Jagora : Duk wanda ya ƙuna gobe,
: Shi ya ɗauko kan kare nai.

Idan aka yi la'akari da wannan waƙa a za a fahimci, cewa waƙar ta na magana ne, a kan cewa duk wanda ka ga ya shiga wuta a lahira, aikin da ya aikata ne ya kai shi, wannan waƙa sai ta dace da abin da Musulunci yake magana a kai cewa duk wanda ya shiga wuta

sakamakon aikin da ya aikata ne, saboda haka a kirar waka Bamagujiya ce amma a ma'ana Musulma ce, don an sami abubuwan da suka da ce da Musulunci, ko kuma suka da ce da shi.

4.0 Kammalawa:

Wannan makala ta bayyana yadda ake iya samun wakar baka ta Hausa ta zama dauke da batutuwa wadanda suke da alaka da Musulunci ta kut-da-kut domin wani loto idan wakar baka ta bayyana wani bayani sai ka ga kamar ta fassara wani zance na Allah, madaukaki, ko na Manzon tsira. Duk da cewa wasu na ganin wakar baka ai sai nishadi, amma ba haka abin yake kawai ba, ga misalai nan dai gwargwado da wannan takarda ta kawo.

Wannan ya nuna ke nan yawanci wakokin baka wadanda ake rerawa za a tarar suna dauke da wasu halaye na Musulunci, musamman ganin al'ummar da ake yi wa wakokin Musulma ce.

Manazarta

Abubakar, H. S. 1991. 'Shehu Ajilo Danguzuri: Rayuwarsa da Ayyukansa" . Kundin Digirin Farko. Kano: Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Adamu, M. 1978. *The Hausa Factor in West African History.* Zaria: Ahmadu Bello University Press - Ibadan: Oxford University Press

Dangambo, A. 2007. *Daurayar Gadon Fede Waka.* Zaria: Amana Publishers Limited.

Ɗangambo, A. 2008. *Rabe-Raben Adabin Hausa.* Zaria: Amana Publishers Limited.

Gumi, A. M. 1982. *Alkur'ani Mai Girma.* Tarjamar Ma'anoninsa. Beirut, Lebanon: Dar al Arabia.

Gusau, S. M. 2003. *Jagoran Nazarin Waƙar Baka.* Kano : Benchmark Publishers Limited.

Gusau, S. M. 2008. *Dabarun Nazarin Adabin Hausa.* Kano: Benchmark Publishers Limited.

Gusau, S. M. 2008. *Wakokin Baka a Kasar Hausa: Yaneye-Yaneyensu da Sigoginsu.* Kano: Benchmark Publishers Limited.

Magaji, M. Y. 1983 . "Wakeƙeniya" Kundin Digirin Farko. Zariya: Sashen Harsunan Nijeriya da Afrika, Jami'ar Ahmadu Bello.

Umar, M. B. 1987. Ɗanmaraya Jos da Wakokinsa. Ibadan: University Press Limited.